[17/07, 17:32] JAMILA Katin: 💧💧💧💧💧💧

*WANI BURI*
💧💧💧💧💧💧

```TYPING```✍🏻

*ON 25 JUNE  2020*

*ALHAMDILILLAH!*

````DUKKAN YABO DA GODIYA SI TABBATA GA ALLAH SUBAHNAHU WAta ALA````

```SPICIAL DIDECATED
TO MAMAN ZAHRA AND DAUGHTER AMMI```💕 Love u so much

*STORY*
Nana fiddausi

PAGE1️⃣▶️2️⃣

"masoyiyata babban farin cikina kuma abinda yake raina nake ta burin ganin tabbatuwarsa shine ganin ranar auran mu"sahabi kenan nima yanzu abinda nake buri gani    kenan" Huzaiyya tasa hannu ta rufe fuskarta alamar jin kunyar maganar da tayi Adiyya ce tazo zata shiga gida ta farayiwa sahabi kirarin dayake sanyashi yimata kyauta jaka guda cikin yanayin barkwanci ta fara cewa "yayi  babban yaya manya abaku naku daban kaga maigidan Huzaiyya eyye angon Huzaiyya sannan baban yaranta da sauri yasa hannu a aljinu yana washe baki ya ɗakko jaka guda sabu dal ya miƙawa wa Adiyya yace" gata kin cancanci inbaki fiye ma da haka domin kuwa duk duniya bani da masoyin daya fice maisan aure na da Huzaiyya" ita dai Huzaiyya najinsu batace komiba kasancewar kunsan mutanan kauye da tsananin kunya.

Huzaiyya ce ke tafiya rafi ita da ƙanwarta Adiyya hannu guda riƙe da kayan wanki a c. k boket hannu guda kuma rike da tulun ɗibar ruwa, Adiyya sarkin hira dan gaskiya Adiyya tana da yawan magana saɓanin yar uwarta Huzaiyya da batacika yawan surutu ba, takalli  yayar tata tace "yaya Huzaiyya gaskiya kinyi sa a domin kuwa yaya Sahbi na matuƙar kaunarki sannan gaba ɗaya kauyen tulunkalwa  babu wani matashi maiji da kyau waye ilimi kuɗi da kuma nasaba kamar yaya Sahbi gaskiya ina matuƙar maki murna da samun kamarsa"  mumrmushi Huzaiyya tayi wanda yafito da kyauwunta da kuma  beouty piont ɗinta mai ƙarawa chaculete ɗin
```

fuskarta kyau tace"nagode Adiyya kema Allah kawo maki miji nagari"  haka suka isa suna tahirar soyayyar  Huzaiyya da Sahbi.

*SAHABI*
Sahbi ɗane ga wani attajirin mutum a cikin kauyen tulunƙalwa inda duk wanda ya kwana yatashi a kauyen yasan da zamansa da kuma tarin dukiyarsa yana da yara guda biyu duka maza bashi yana da mata wadda kullum cikin faɗa suke tana faman yaji wanda ba wanda yasan abinda yake yawan haɗasu fitanar  again itace mahaifiya ga Sahbi da kaninsa Aminu
Sahbi yana matuƙar qaunar Huzaiyya irin kaunar nan daza a iyabada kwatancanta a  ko ina agamsu bama Huzaiyyaba masoyan Huzaiyya ma in Sahbi gani baya barinsu haka yanajin zai iya ƙarar da duk abinda suka mallaka adoran duniya indai akan soyayyar Huzaiyya ne shikam yasan bai faɗi ba. yana da aboki guda ɗaya Anas, ra ayinsu yazo ɗaya da Sahbi domin Sahbi mutum ne mai zuciya da takaici bashi da shashanci yana da maida kai akan duk abinda yasanya agabansa yakansa hakuri da juriya jajurcewa da kuma addu a hakan yasa abubuwa kaɗanne bayayin nasara akai shiyasa tasu tazo ɗaya da Anas domin shima sunanan suna kauyene ne amma bashi da duhun kai ko mutuwar zuciya bare shashanci.

wanke wanke takeyi tana ƴan wake wakenta inda Inna Barira ka ƙaraso tana cewa" Adiyya maza kigama in aike ki gidan mallam Tanimu gurin Afshe kikaimata kuɗin dashi kai taɗago "haba Inna kinga wanke wanke   nakeyi amman ga yaya Huzaiyya nan bata ta miƙa"  Huzaiyya dake ɗaki tanajinsu tayi maza ta fito tace  " Inna kawo namiƙa mata" tasan abinda ya hana Innar ta aiketa tun wuri saboda tasan gidan su Sahbi ne bata kuma san zuwa amman zata daure kodan kara da yawan karamcin Inna Batiri ga rayuwarta ta mata komi ta inganta rayuwarta kamar daman ita ta haifeta tunda ta tabbata marainiya bata kukan maraici saida kukan rashin uwa da uba amman Inna Barira ta haɗadu duka tariƙe kamar ita ta haifesu hakan yasa bata taɓa bijirewa Inna ko barin Inna dadamuwa da tamata gata da dukkan alkairi.
amsar kuɗin tayi tasanya hijabinta tana cewa" saina dawo Inna" tafiya take kasancewar lokacin damunane kuma jiya antafa ruwa ƙasa tajiƙe gari sai kamshi lema yakeyi yayinda bishiyoyi suka juku sukayi gwanin kyau tsirrai sunfito sunyi lif yayinda hatsi duk ya fidda kai a gonaki haka take tafiya a hankali kamar mai tsoron taka ƙasa tana fice gonaki masu cike da albarkatun gona ga tsanwaye shar gwanin sha awa.

sallama tayi tayi amman ba a amsama mata ba da ƙarahe jitayi anfito anfisgeta anjefa ɗaki anrufo ƙofa haka tayi tazabga ihu ba maijinta

haka tanaji tana gani tana ihu tana komi aka afka mata inda akayi disvargin ɗinta da ƙarfin tuwo aka rabata da martabarta  dasha kuka bakaɗanba

tunda tatabbatar anɗagata tayi sauri ya ja jiki tana ta faman murzar kuka tafito tana har harɗe ƙafa ƙamar zata faɗi wani irin raɗaɗin azaba takeji a ƙarƙashinta sai da ta shiga cikin gonaki

tasami wata bishiyar  limis ta zauna takifa kanta akan gwaiwarta tana ta rigar kuka a haka iska da danahin gurin suka saukar mata da kasala inda batsan sanda barci yayi awon gaba da ita anan ba .

cikin barcin ma mafarkin abinda ya faru da ita tayi inda ta farka afirgice zata kwalla ihu baki taji an rufe mata kiciniyar kwacewa takeyi a hankali yace" haba Huzaiyya miyasa zakizo nan kikwanta baki tsoron wani abu ya cutar mani dake anan gurin  inba dan Aminu ya ganki yaje yasanar danoba da komi zai iya faruwa wai ma miyasa kike kuka ɗazu Aminu yace mani yaganki kina kuka???" yana tambayarta dasan ƙarin bauani cikin tsananin damuwa bil haƙƙi ita kuwa bata lura da Aminun ba kuma bata daniyar kokallansa bare tabashi amsa tashi tayi tana harhaɗe ƙafafuwantanta tana ƙoƙarin tafiya mamaki ya kama  Sahbi yace"Huzaiyya Sahbinkine ke maki magana" banza tayi sashi zatayi gaba yayi maza yasha gabanta cikin kuka tace" kasan Allah inbaka matsamin hanya na wuce ba yanzu zanma ihu kwarto!" agurinan mamaki yakama Sahbi kodai wani abu tasha sannan ganin dadik gaskiyarta tayi maganar yasa yayi maza ya matsa amman kanshi ya ɗaure

zaune take gaban madubi tana shfa man  *NIVEA* na campany gucci a hankali takebin sannan jikinta mai yawalwattacan kyau da da lafiya take shafewa zuciyar ta kuwa cike da ɗoki zuwa ga cikar *burinta* haka ta tsaya ta tsara kwalliya ta mussaban da burge   Taupiq  cikin wata fadi ɗin shadda milk color wadda aka yiwa aiki da pink ɗin zare wani cover sheos tasa pink mai zallar kyau wanda akayiwa ado da golden band ɗin kanta da abin hannu sarka da ƴan kunne duka pink da adan golden lip ɗinta yadau lip sectek sai walkiya yake turaran gucci blood ta fisa inda jikinta yasha humra da kulacca da shuwa da body spray masu daɗi daka kalleta kaga babbar yarinya duk wanda ya ci yatada kai zaiso ya huta da kuruciyar yarinyar da kuma lafiyarta domin tayi takowwane gefe fitowa tayi tana "cewa oum na sai nadawo  nasiha oum na mata sannan ta mata fatan alkairi inda ta nufi ƙayattaccan  garden ɗin gidan inda suka saba hira da sanyin idaniyarta *Taupiq*

*Pls dont forget shared and comment*

*Nanah Fiddausi*
[17/07, 17:32] JAMILA Katin: .💧💧💧💧💧
*WANI BURI*
💧💧💧💧💧

TYPING✍🏻

*ON 29 JUNE MONDAY  2020*

```SPICIAL DIDECATED TO
MAMAN ZAHRA AND DAUGHTER AMMI```💕
```

*STORY*
Nanah ibrahim

*بسم الله الرحمن الرحيم*

⚖
*HOME OF QUALITIE'S WRITER'S ASSO📚*
```{{The Home Of Qualitative Writers That Are Educate Humanities}}```
https://m.facebook.com/story.php?story_fbid=106249334371950&substory_index=0&id=106248871038663&sfnsn=mo

*⚜{{H.Q.W.A📚}}*

_SEASON_ 4

……Hannayenta  ta kama ta riƙe a gaban cikinta idanuwanta ta ɗago tana kallan fuskarsa cike da tausayi itama hawayan ya fara sauka a saman kuncinta,  ido ya kura mata yana matsowa kusa da ita a hankali ya durkusa bisa gwaiwowinsa ya fara magana bakinsa na rawa yace "Adiyya Huzaiyya bata zuwa ko????" miƙewa yayi yana kakkaɓe hannayansa daya dafa a ƙasa yaci gaba da cewa  "bansan minayiwa Huzaiyya ba ta juya mani baya tsaneni bata sona narasa dalili!" magana yake cikin damuwa wata kan wata inda Adiyya ta cigaba da kallansa kamar pic yayinda hawaye yaci gaba da kwarara a saman fuskarta cikin sayin murya fara magana yaya Sahbi kayi hakuri komi mukaddarine in Adda taƙika wata za taso...."bata ƙarasa ba ya juya da sauri yabar kofar gidan yana sa hannu a kunne yana toshe kunnansa alamu baya sanji.

maraicene mai cike da sanyin damina  inda biyoyi ke kaɗawa inda garin mai tarin ni imar yalwar saiwar itace masu saukar da nutsuwa a yanayi rani sai kaɗawa suke ,cikin yanayinta daya zama identity ɗinta tana tafiya rungume da alkur ani a hannunta mai rubutu warash  tun bayan faruwar abin bata da wani sukuni kullum cikin damuwa take ga chanzawar lafiya  ajikinta   da takeji direct gurin Idi mai tireda tanufa  sallama ta mashi ya amsa yana cewa"Malama Huzaiyya kin ƙaraso har an tashi ya karatu???? kinsan kawun nan naki yadamu da sanjinki  bara ingama inmashi filashin sai kuyi magana" kai taɗaga mashi tsaf ya gama jere kayan tiredar sannan yace "yawwa barana mashi ko" yana magana hankalinsa akan sweet ɗin dake gyarawa zama .

hira sukayi da   kawu Lauwali kamar yadda ake kiransa a kauyan na tulunkalwa  sosai kamar bada credit a keyin wayar ba kewar ɗiyar ƙanwar tasa yakeji ji yake kamar yayi tsuntsuwa yazo kauyan ya ganta itama kuma a halin yanzu tana cikin kaɗaici da damuwar rashin ma kusanci shiyasa ta kejin itama kewa dasan ganin waninta a kusa da ita, duk kuwa da cewar gaskiya
```

Inna bata rageta da komi ba basuyi sallama ba saida yayi mata alƙawarin zuwa last mouth insha Allah.

wasu hawaye suka zubo mata wanda tun bayan faruwar abin takeda tabbas ɗin akwai wani abu mai muni dazai faru ga rayuwarta ga matsananciyar soyayyar Sahbi data addabi ruhinta.
tafiya takeyi ciki gonar inda tadau hanyar gida kasancewar gidajan garin duk a haɗe suke da gonaki Aminu ne ƙanin Sahbi ya tsaida ita da fara a domin daman mutuniyarsa ce dan yana kaunar auran yayansa da Huzzayya yace " Adda Huzaiyya sai ina?" tana ƙoƙarin bashi amsa ta hango Sahbi da sauri ta juya da nufin tafiya shima da sauri ya bita gefan hijab ɗinta ya kama yace" wai mekike nufi Huzaiyya? ina ɗinbin kaunar dakike ikirarin kina mani?  dama yaudara takike ko shin kinsan irin halin da kike ƙoƙari jefa rayuwa kuwa ? haba Huzaiyya kada kikunyata kauna kada ki juyawa masoyinki baya ki gayamin lefina zanzamo maineman yafiya ina kuma roƙonki kizama maiyafiya yayinda nakasance mai lefi agareki "yaƙarashe maganar yana kama kunnuwansa  kuka tafashe dashi tana fizge hijab ɗinta da sauri tayi gaba duk abinda sukeyi Aminu na kallansu wata kwallar tausayin ɗan uwansa tazibo mashi a domin yasan irin macewar da ɗan uwannasa guda ɗaya yayi akanta hankali Sahbi ya isa kusa dashi yasa hannu yana goge mashi hawayan shima idansa na fitar da kwallah tausayin kansa suna ciki haka sukajiyo wani gigitacan ƙara inda suka tabbatar da Huzaiyya ce da sauri suka bazama suna zuwa sukaga wasu kwailayene suke ƙoƙarin haye mata da sauri Sahbi ya tube ya fara gabzarsu inda ba aje ko ina ba ya masu raga raga wasu kuma sunga zasu sha wahala suka ari takare. hannuwanta yakama yana duba ko ina najikinta up to down idanuwanta ke yawo aka kyakyawar halittarsa tun daga sama har ƙasa kirarsa kamar ta larabawa kyauwunsa kamar bana jinsin Hausa ba yafi kama da ƙabilar larabawa ko  fulani masu tsantsar kyau hawaye yazibo mata datatuna ta rasashi data tuna illar da ke jikinta tafi wadda yake nema tanaji tana gani zatayi asarar wannan gwarzon matashi, dara daran idanuwansa masu haske kamar tocilan ya ɗago yana cigaba da ƙare mata kallo inda ita kuma ta sadde kai ƙasa

*Pls comment and share*

Nana ce
[17/07, 17:32] JAMILA Katin: 💧💧💧💧
*WANI BURI*
💧💧💧💧

TYPING✍🏻

*ON*

*MONDAY6 JULY/72020*

```SPICIAL DIDECATED TO MAMAN ZAHRA AND DAUGHTER AMMI```💕 Love u so much

*STORY*
Nanah

_SESION SIX_

*بسم الله الرحمن الرحيم*

⚖
*HOME OF QUALITIE'S WRITER'S ASSO📚*
```{{The Home Of Qualitative Writers That Are Educate Humanities}}```
https://m.facebook.com/story.php?story_fbid=106249334371950&substory_index=0&id=106248871038663&sfnsn=mo

*⚜{{H.Q.W.A📚}}*

........Ajiyar zuciya Kawu ya sauke yayinda ya ɗan fesar da iska ta bakinsa yace"Barira kinsan halin yaran zamani tunda yarinyar ga taƙi to mubarta tunda dama susuka shirya kansu kinga bamu da masaniya akan dalilin ƙin amincewarta wata ƙila tana dadalili" Inna itama dai nisawa tayi dan wannan kawai sai yazama abin kunya agurinsu ƴan ƙauye domin abin kunya baya kaɗan a ƙauye.

tace Lauwali kana ganin ba matsala yace "eh tashi yayi yana mata sallama zai koma amman insha Allah nan kusa zai dawo akwai abinda yayanke amman zai je ya fara daga can. haka ya mata sallama yatafi sanda ya fito har ya kama murfin car ɗin zai rufe Huzaiyya tafito da sauri har tana tuntuɓe, hannu take ɗaga mashi daga kƙofar gidan kofar motar yabuɗe ta baya alama ya mata data shigo shiga tayi magana ya fara mata cikin sigar lallashi yace"Huzaiyya nasani a rayuwa kowanne bawa da irin kaddurarsa ina baki hakuri da kiyi hakuri da lamurranki duk da bansan damuwarki ba bazan tsananta ba amman idan nayanke hukunci akanki any way banasan ki watsa mani ƙasa a ido kai ta ɗaga alama gamsu nasiha sosai ya mata sukayi sallama ya tafi.

zaune yake a porlour yana rubuce rubuce inda yake lissafin abinda aka rasa a kasuwar wannan satin momi ce take cewa "Dad ɗin Taufiq kada kazama mai halin ƴan kasuwa mana idan ansami

riba shuru inkuma ansami faɗuwa jaje" cikin barkwanci tayi maganar inda ya ɗan ɗago idansa wanda ke dauke da siririn tabarau yaɗan girgiza kai.

cikin wasu lafiyayyun T shert da trozer sky blue  fuskarsa kamar Dad ɗinsa sanye da tabarau shima launin sararin samaniya  kamshi jikinsa mai daɗi da sanya nutsuwa ya fara shigo cikin porlour ɗin  sallama ya masu inda ya zauna kan wata rest cheir dake gurin cikin nutsuwa ya gaida momi sannan ya gaida Dad ɗin bayan ya gama gaidasu Dad yace masa Taufiq ya kamata fa ka girma haka kansa yaɗan sosa inda ya ƙara sadda kai yana ɗan satar kallan iyayan nasa sannan daga bisani yace"am daman Dad inaso ingaya maka munriga da munga magana da Hadiya nama gaya mata zakaje gidansukan batun"  ɗan gyara zama  Dad yayi sannan yace "banganeba wace yarinya kake nufi kennan?" Momi tace "haba Dadyn Taufiq yakake magana kamar bakasan cewa yana neman yarinyar ba aikasan da maganar ta"
haɗe ransa Dad yayi yace "eh nasanda maganarta kuma za ayi tata amman yanzu nasama mashi matar aure amman dayake shi mijin mace huɗune ko bayan ya auri wannan ɗin daga baya sai ya auri ita Hadiyar amman bisa sharaɗi ɗaya shine ya tabbatar zai adalci"

Dariya Momi tayi tace"wai dan Allah Dad ɗin Taufiq miyasa kake dasan zolayane miyasa kake da abin mamaki?  sai ana maganar gaske kuma sai kakawo wasa miyasa?"
kallanta yayi serious yace "kamar ya wasa in rasa da wanda zanyi wasa sai My son kuma a irin maganar nan kina tunanin zan sanya wasa a cikinta? to kinyikuskuran fahimta  ya canza akalar zancannashi da cewa Taufiq ya amsa na am Dad inaso kasani ni mahaifinka nazaɓa maka mata kuma ba kowa bace face Huzzayya ƴar ƙanwata ramla marigayiya sannan inaso kashirya kaje kugana dan sati biyu kacal za a sanya  shiyasa nakeso kaje kaganta umarnine  nabaka yana gama faɗar haka ya miƙe Momi baki da hanci tasaki tana mai matuƙar mamakinsa daman da gaske anayiwa Namiji auran dole yau zataga abinda ya shallake tunaninta.
ɓangaran Taufiq kuwa mamakine ya cikashi fatansa ya farka daga mummunanan mafarkinsa mai firgita masa tunani haka ya dinga mursa idansa amman me sai ya tabbata aleave abin yake faruwa.

miƙwa yayi bai cewa Momi komi ba ya fice itama Momin tashi tayi tayi ciki.
sosai Dad yake duk wani shiri duk da yasan cewa har yanzu Taufiq baije ƙauyan ba  gashi yau kwana huɗu dayin maganar yanzu kam yayanke shawarar zuwa yasami dangin mahaifin Huzaiyya zai bayar da sadaki daga baya aje ayi  a daura aure yanasa ran tafiya  ganin likitansa totarly one week ya rage shiyasa yakeso kafin ya tafi ayi komi agama.
kwance yake a ɗakinsa juyi yake akan bed ɗin baya iya tuanin komi sai damuwar da Dad ke ƙoƙarin sanyasa acikinta domin shi kam taya za ace za mashi auren dole auranma ƴar ƙauye baya yana da wadda ya dauki burin duniyarsa ya ɗora akanta gaskiya akwai cutarwa agareshi pellow dake hannunsa ya matse a kirjinsa gam yana rufe idansa tsam ya miƙe a bed ɗin rigar wankansa ya sanya bayan ya cire ƙaramin bozer ɗin dake jikinsa toilet ya  cikin kwamin wankan ya shiga rigar wankan ya fdda take ya fara juyi a cikin kumfar data gaji da sinadarin kamshi wa gumi mai daɗi yake ratsa duk wani sassa na jikinsa saida ya gama gasa jikinsa da ruwa ɗimin sannan ya ɗauraye jikinsa ya fita tsaf ya shirya wayoyinsa ya kwasa dake kan bed size saukowa ya farayi daga upsteir's inda Dad da  Mom ke zaune suna hira cikin nishaɗi wani

kululun baƙin ciki ne ya turkinƙe zuciyarsa wato Momi harta manta abinda Dad ɗin yake shirin masa shine har da zama dayin hira har da dariya cikin nutsuwa ya gaidasu sannan ya miƙe zai fita Dad ne ya dakatar dashi dawowa yayi ya zauna yana fuskantarsa kansa a sunkuye ransa namasa zafi dan yasan kwanan zancan Dad "yace  Taufiq kaje kuma kungana da Huzaiyya?"

a hankali yace "a a " yace to bazakaba nan ma gorgiza kai yayi yace kawai Dad bazan gane ƙauyan bane"Dad yace kajiba to da ance za a ƙara haɗa zumunci kaƙi kuma gashi yana ƙoƙarin lalacewa nanma girgiza kai yayi yace no Dad nibance naƙiba yace to shikennan kashirya Kabeer driver   ya kaika to yace tare da cewa ya fita yasa kai ya fita.

a cikin ransa babu daɗi umarnin iyaye kawai yakebi sannan ya tunanin tayaya zai fahimtar da Hadiya wannan batun gashi kuma yanaga sam mahaifinnasa bai gyara masa

sannu hankali motar ke gangawara ciki unguwar su Huzaiyyar parking motar Kabeer yayi a ƙofar gidan inda yake cewa "Oga mun iso kansa ya ɗaga a hankali yana ƙarewa gidan kallo kafin daga bisani ya cewa "Kabeer ya shiga ya sanar da Inna cewa tayi baƙi haka ya shiga bayan sun gaisa a mutumce yake sanar da ita tare suke da Taufiq dayake Inna tasan komi sai tace ya sanar dashi ya shigo daga ciki bayan ya shiga cikin mutunci da kima ya gaida Inna sannan aka turo mashi Huzaiyyar itama ƙarƙashin ranta kamar andoka mata guduma kasancewar Inna tagaya mata komi yayinda Kawu ya gaya mata asakaye. gefen  tabarbar robar da a haka  shinfiɗa mashi ta zauna tana mashi sallama be kalletaba sannan bai ɗago ba shikam bashi da burin sake kallan wata mace a duniya a matsayin mata inba Hadiya ba Adiyya ce ta ajiye kwananan shan ruwan mai cike da ruwan randa a ciki mai sanyi tayi ciki dan bala in haushinsu takeji su duka kuma duk  abinda take Huzaiyya na ankare da ita a hankali kamar maraya ya fara magana "ki adana gaisuwarki  sannan na haɗaki da girman Allah zan iya baki ko nawane a rayuwa ke komi kekeso zan maki amman ki gayawa Dad  cewa bakisona look kinga bamu dace ba after that inada wanda muka daɗe muna da burin kasance wa tare pls bazan iya cin amanar taba taya mazaki iyazama da mutumin da baki sani ba wasu hawaye masu zafi take fiddawa daga idanta yayinda kuma daidai lokacin Aminu yayanke shawarar zuwa gidansu Huzaiyyar ya nemi daidai to agurinta tunda lamarin ɗan uwannasa sai ƙara gaba yake yanzu kam ko abinci baya iya ci yadda ya kamata ga yawan zazzaɓin damuwa shidai burinsa Huzaiyya yana damuwa da irin soyayyar daya afka yana addu'a Allah yaye ba masa koyasami sausauci kamashi" yayi yace  Aminu karkaje "Aminun ma shima cewa yayi Allah Yaya kabarni inje miƙewa yayi yace muje "tare" daidai shigarsu gidan ta goge hawayan fuskarta sannan ta saki wani murmushi mai ciwo
tun kan yaƙarasa shiga yaci karo da  wata mota a ƙofar gidan su Huzaiyya Sahbi ya shiga ciki zauran hawaye ya fara fitarwa a fuskarsa na takaici yafara magana humm yanzu na fara fahimtar dalilinki daman wannan ne dalilin dayasa kika juya mani baya kai ya girgiza hawaye nacigaba da zuba a fuskar sa yace kinyi kuskure Huzaiyya kuɗi zasusa kisaida soyayyar da aka gina a tubalin gaskiya lalle bakiyi tunani ba kuma da wani ya gaya mani haka zan ƙarya amman kije nabarki da Allah ban yafeba.

daidai lokacin ya juya yana girgiza kai ya daɗe yana nacin cikar burinsa ashe *wani burin, baya cika*  Aminu ma take masa baya yayi sukayi gaba inda Huzaiyya ta miƙe tsaye idanta na kwararar da hawaye mai zafi ahima Taufiq miƙewa yayi da mamaki

_pl comment
&shared Nanarku ce_
[17/07, 17:32] JAMILA Katin: 💧💧💧💧💧
*WANI BURI*
💧💧💧💧💧

*ON 24 JUNE 2020*

```SPICIAL DIDECATED TO```
```Maman zahra and daughter Ammi```💕Love u  so much

_Shafin duka kyautarwa ne ga ƴan home of quality writter's ana lukutar tare_

*STORY*
Nanah Fiddausi

_SESION THERY_

.......... Tafiya  takeyi cikin nutsuwa jikinta sai juyi yake wani kamshi mai sanya zuciya nutsuwa yake tashi daga nahiyar da take tahowa.

Zaune yake cikin garden ɗin tun daga nesa ta hangoshi tundaga kan ƙafarsa ta fara kallansa har zuwa saman fuskarsa sanye yake cikin kananun kaya ƙirar campany gucci riga da wando ne marrom  colour  gabansu wani adan flawer ne anyi mashi ado mai kyau da farin zare saman kansa hula ce facing cap itama maroom  ƙafarsa ma sanye take cikin  cikin wani haɗaɗɗan plant sheos ƙasan sa farine samansa marrom  colour    aai maiƙo yake sumar kansa da sha askin zamani sannan tasha gyra da camb da mayuka masu matuƙar da  Taupiq kennan cikin siroroyar murya Hadiyya ta mashi sallama  a hankali wadataccan iskan ke kaɗawa inda yake kaiwa hancinsu daddaɗan kamshin jikinsu tare suka lumshe idanuwa suka  bude a hankali ya miƙe cikin issa da isa ya amsa sallamar amman idan ba kakalli bakinsaba bazaka taɓa cewa yana motswaba balle makayi tunanin ya amsa hannayansa ya buɗe inda tatafi da sauri ta faɗa ya rufe  tare suka sauke  ajiyar zuciya  tare dajin  wani sanyi a ƙarƙashin zuciyarsu  haka suke fatan kasance abadan sun dauki lokaci maitsawo a haka Hadiyya ta fara janye jikinta inda Taufiq ya kama hannunta ya zaunar da ita yana mai lumshe idanuwa duka gaisuwar tasu da turanci sukayita sanda suka juya harshe inba kasan cewa da ƴan asalin west africa bane bazakata cewa ƴan Nigeria ga bane  bayan ta zuba mashi abin sha dangin su 5 Alive coconut

juice  dan tasan shiba gwanin abubuwa masu nauyi bane a hankali wasu tsutsaye suka dinga shawagi agurin inda ya ɗaga kansa yashagala da kallansu tasani a rayuwar Taufiq mutum ne shi mai matuƙar sha awar kallan tsuntsaye da ɗawisu yana san ƙananan halitu sannan shi mutum ne maisan shuru da kaɗaici bayasan hayaniya miskiline na bugawa a media  yanasan soyayya da ganin masoya yana bayawa masoya gudunmawa ko ina suke dan gudanar da qauna cikin sakewa yana girmamam so da *miradin zuciya*  sunanan buk ɗin Autar manya abinda kuma Taufiq bayaso shine asanyashi yin dole a inda bashi dadamar bijirewa bayasan yaji ko a labari ance za ayiwa mutum auran ƙiyayya ko kuma dole wani tsuntsune kamar yasan abinda yake zuciyar Taufiq yazo kusa da Taufiq yana wani irin kuka mai daɗin sauraro inda Taufiq ya kashe kunnuwansa yana saurara Hadiyya tasani ko sanda suna east Africa  babu abinda ke birge Taufiq like this moment kallanta yayi yace " angle inasan tsutsaye" ya furta ahankali murmushi tayi wanda yayi matuƙar bayyana kyauwunta tace" nasani" Hadiyya tana matuƙar birge Taufiq domin bata da hayani kamarshi komi nasu yana shige bata tsawaita magana kaf makarantarsu babu namijin da ta iya bawa haɗin kai kamar shi domin taga ra ayi sanda yatanka mata ta amince dashine domin tana ganin rayuwarsu zatazo ɗaya domin yasan hkkin so da kuma ɗan Adam  haka hirar tasu takasance cikin miskilanci domin miskilai  2 ne suka haɗu hakan yasa zama yafi hirar yawa.

Lokacin da Sahbi yaga Huzaiyya zata haukace mashi sai yabata hanya tatafi badan yaso ba amman kuma zuciyarshi cike da tunani iri iri wai yau shi Huzaiyya keyi ma tsawa harda kiransa da kwarto miyasa??? .

Tafiya take tana harharɗewa a haka harta isa gida inda Allah ya taimaketa babu kowa agida Inna da Adiyya suntafi gidan Mallam ɗalha barka haka tayi sauri ta faɗa ban ɗaki boket ta cika da ruwan randa tayi magewaya da sauri tacire kayanta duk suɓaci da jini tawankesu tas da omo sannan ta dauki soso ta fara dirzar jikinta yawa zata cire abinda yafaru, bayan tagama sannan tayi wankan tsarki tafito tana matse ƙafafuwa saboda masifar azabar da takeji da sauri tashige ɗaki rab ta dauka ta buɗe jikinta tadinga shafawa wai ko zataji sa ida nan kuwa zafi ya ƙara cewa salama alaikum kuka take mai sauti tana ambatan Allah da tunanin mutuwa nagab da daukarta ta huta  a haka wani irin wahalallan barci ya kwasheta.

Cikin barcin taji  Adiyya natashinta zuwa lokacin zazzaɓi ya rufeta maitsanani hannu Adiyya takai bisa wuyanta da sauri ta janye tana cewa "Adda  Huzaiyya miyasameki"!?  ido tabuɗe hankali tana kallanta wasu hawaye masu zafi suka zubo mata tace" bakomi kawai dai aazzaɓi kedamuna"
dasauri Adiyya tafita tana gayama Inna zananta takunce  ta ciro  naira ashirin tace"maza kije guri Idi mai tireda kisayo mata magani!" taƙarasa maganar cikin damuwa da sauri Adiyya tafita kamar zata kifa dan sauri ta siyo maganin takawo mata ruwa ta dauka aranda tatafi da sauri gurinta a hankali take" cewa Ada tashi kisha magani" hannu tasa tataimaka mata tatashi daga kwanciyar da tayi ta kara mata kofin maganin ta fiddo daga cikin gidansa ta zuba mata abaki tabi da ruwa kuka takeyi sosai inda Inna take mamaki takuma ruɗe kan ganin yadda tashiga cikin mawuyacin hali tasan tabbas ba ƙaramar lalura bace zata sanya Huzaiyya kuka ita kuwa

azahiri kuka takeyi ana ganin kamar rashin lafiyarne yasanyata kuka wanda abaɗini bashi takeyiwa kuka ba kawai tana kukan mummunar *kaddarar data afkawa rayuwar ayau* haka sukayi taƙoƙarin ganin tayi shuru ita kiwa tana ganin kukanshine mafi alkairi agareta.

Daddadare saiga yaro Sahbi na sallama da Huzaiyya aransa yana saƙa yanzu yasan tadawo nutsuwarta zataji kunyar abinda ta mashi ɗazu amman gaskiya tasanyashi damuwa bakaɗanba ana cikin tunani ya tsinci muryar yaran nashaida mashi wai tace bata zuwa acan cikin gidan kuma Inna sai faɗa takeyiwa Huzaiyya taya zatace mashi bata zuwa kawai tace mashi batajin daɗi ita dai Huzaiyyar batayi magana ba shuru tayi tarabu da Innar  yayinda Adiyya tafita da sauri gurin  Sahbi tashida mashi Huzaiyyar kebata da lafiya da sauri yace"misameta!?" harshansa  har yana harɗewa Adiyya tace "mashi zazzaɓine ke damunta amman nasiyo mata mag......" bai wani baribta ƙarasaba ya banka cikin gida Inna ya fara cinkaro da ita cikin jin kunya yagaida Innar itama cikin ji n kunya ta amsa mashi inda ya isa gurin Huzaiyya yayi yayi tamashi magana taƙi inda yake ganin kamar zafin ciwone yanata magana ranar kamar yayi hauka sannan bayan ya koma gida kasa runtsawa yayi da idansa.

a hankali damuwa takeyin yawa ga Huzaiyya inda kullum idanta baya rabuwa da hawaye, kaf gidan sunkasa gane mata moment ɗin gidan ya chanza babu farin cikin ba walwala kodayaushe gidan yadawo damuwa sak.

yanzu ma Adiyya ce durkushe gabanta tace "Adda Huzaiyya inhar bakici abincinan ba wallah nima bazanci ba domin na lura kinfiso kiga hankali kowa yatashi agidannan baki san kwanciyar hankalimu idan har bazaki iya gayama damuwarki ba to ki maido farin cikin gidanmu kiriƙe damuwar tunda munyi munyi kigaya mana damuwarki kinƙi ni adamuwa Inna adamuwa sannan gaba ɗaya kin juyawa yaya Sahbi baya yanzu haka maganar danake maki bashi da lafiya kuma duk dalilin juya mashi bayan dakikayi!"

tana rufe bakinta yaro yashigo da sallamarsa wai Sahbi na magana da Huzaiyya Adiyya takalli yaran tace" kaje kace tana zuwa" hannun Huzaiyya takama tace dan Allah kidaure ki saurareshi da sauri Huzaiyya ta girgiza mata kai acikin fushi da kunar zuci Adiyya ta miƙe tanufi ƙofa gurin Sahbi tana isa Sahbi ya fara mata hawaye yana roƙonta ta taimaka tashawo mashi kan Huzaiyya ko tagaya mashi  lefin daya mata ta juya mashi baya"
[17/07, 17:32] JAMILA Katin: 💧💧💧💧
*WANI BURI*
💧💧💧💧

*ON*
*13/JULY/7/2020*

_SPICIAL DIDECATED TO MAMAN ZAHRA AND DAUGHTER AMMI_
Love u so much💕

```gaba ɗaya shafin sadaukarwa ne gareki Fa eezation Maman Abdul da ummu Sahiba ta Allah ya bar kauna```💕

_SESION  8_

_Kukan zuciya zafi biyu  da kuma damuwar zukata!_❣️💘

*2 HOT*

............ Suna isa Doctor Fa iza ce ta amshe ta  ita ta fara dubata a lab direct doctor yasa aka nufi lab da ita dan auna jininta da fitsari, bayan an auna jinin Taufiq a dankewa sakamakon wanda dole tasashi tsayawa domin tunda suka sanar da Dad cewa Huzaiyya ba lafiya suna hanyar Hospital Taufiq da Momi sun amsa wayar Dad ya kai sau goma.
dan haka ya shafawa kansa lafiya ya zauna ayi komi dashi dan inya kuskure yanzu tashi zatayi zafi shi kuma bayan san fishin ɗaya daga cikinsu kunnansa manne da eirpiece  zaune yake yana karkaɗa ƙafarsa akan cheir ɗin Hospital ɗin doctor  Fa iza ce tafito tana wani murmushi ta nufeshi aranta tana mamakin mazan zamanin nan da suke iya auran yara ƙanana wani lamarin Allah nan da nan sai kagansu da juna biyu.

takardar ta miƙa masa tana cewa "congratulation oga"  wani kafirin kallo ya bita dashi amman sai ya dake ya ya amsa, da Momi ta iso gareshi tana cewa" ya akayi My Son mike damanta?" dadamuwa a kan fuskarsa ya ɗago yana kallan Mom ɗin tasa wadda ya kasa furta mata kalma ɗaya bayasan ya sanar da ita abinda ake ciki a gurin nan dan haka yace "Mom ina take?" tace tana ciki " yace "ok    kusameni a mota ya juya yabar resaption ɗin.
 jefar da pepar yayi yanajin wani irin zogi a zuciyarsa tafasa take kamar zata fashe ya duba paper ɗin yakai sau goma tunaninsa ko ƙarya idansa ke nuna masa.

maleria fiver negative
typiod fiver negative
amman kuma wannan gwajin na ƙarshe shine yake nuna positive wato awayo ciki kuma har 4 mouth way? anya ma gaskiya ne?

inhar bai manta ba yau  2mouth da ɗaura masu aure sannan tunda akayi bai taɓa kallanta a matsayin mata ba domin yana ganin bata ma isa auran ba kwata 2 sannan shi bashi da wani nishaɗi tunda yasan kansa face barci ko kuma cin abinci sai kallan furanni da kuma san kukan tsuntsaye wani lokacin yakan kallin wasan ball idan yana da time kan au media domin samun wayewar kai da abubuwan sha awa da kuma na rayuwa amman bai taɓa sanin miye nishaɗin kasancewa da mace ba gara kwanan nan faruwar auransa da yarinyar yakanyi romance ɗin
```

Hadiya dan kwantar mata da hankali lokuta da dama yakan sami kansa cikin mawuyacin felling yakan haɗa ƙananan dibaru da fama da zafin ciwon mara na lokaci daga baya abin ya sakeshi yaci gaba da uzurinshi amman taya ya auri lalattata kuma wadda ba zaɓinshi ya akayi kaddara tazo mashi a haka? kansa yasara waya cutar dashi sitearing ya buga wanda daidai lokacin kuma Momi da Huzaiyya suka ƙaraso gaban Momi ya faɗi ganin wani gumi dayake fitarwa.

acikin tashin hankali da nuna kulawa tace"Son lafiya kuwa?" baiyi magana ba yayi wa motar key ya cillata saman titi.

 suna isa ya miƙawa Mom paper ɗin yayi up dan wani iri kansa yayi zuciyarsa na zafi sannan kuma baya iya fahimtar komi gashi yakasa tunanin madafa.
cikin wani irin firgici Mom ta ɗago da kanta domin da fari dataga positive farin ciki ya rufeta amman kuma ganin watanni cikin yasa murnarta komawa ciki.

cikin tashin hankali tace"Huzaiyya taya haka ta faru!?"

batama jirata ta miƙe bedroom ta shiga ta fara sintiri inhar bata mantaba inhar zatayiwa Son adalci kwata kwata auranma gaba ɗayansa da nemansa da daurashi duka duka wata 3 mouth ne da ƴan kwananaki taya zata kawoshi aranta wanda yanzu cikin yana cikin wata na 4 zuface ta karyo mata inda tayi zaman taɓaro akan bed ɗin tana tunanin lamarin hankalinta a matuƙar tashe.

ɓangare guda kuwa Huzaiyya wani irin raɗaɗi takeji inda tunda ta zauna a gurin motsi ma batayi ba tana matuƙar cikin damuwa idanta ya soye zuciyarta ta bushe kanta ya cunkunshe babu wata kofa dazatayi tunani mai kyau ranta tab da zullumin lamarin yayinda ta riga tayarda cewa babu wata rana da zatazo tasakeyin farin ciki.

wani tunani yazo zuciyarta lokacin da Sahbi yake cewa Huzaiyya in mukayi aure yara nawa zamu haifa? hannu tasa ta rufe face ɗinta tace wana kakeso? yace goma ido ta zaro tana rugawa dagudu inda ya fara samar mata murmushin jin daɗin kunyar ta mai bashi sha awa aikuwa tana gama tunanin waau hawaye masu ɗumi suka gangaro mata a saman kuncinta inda tasa hannu ta share ta kuma ji sauƙin nauyin da kirjinta keyi mata.

wani irin murɗawa cikinta ke mata inda gaba ɗaya ta fita hayyacinta hakan kuma yayi daidai da wani irin murɗawa da yayi inda wani abu mai matuƙar zafi yazubo mata take ta kwalla wani ƙara ta zube saman  kafet ɗin porlour'n sumamma

Sahbi tunda abin ya faru basi da kwanciyar hankali ko nutsuwa kullum  cikin sambatu kwata bashi da lafiya ɗan gayun ma dayakeyi yanzu ya daina baya cin abinci baya wadataccan barci sannan gayawan ciwon kai sabosda damuwa ko yanzu zaune suke ga Umman shi da babansa Umman ce ke mashi nasiha  tana bashi hakuri game da lamarin rayuwa yazama mai ɗaukar kaddara kosa ya kada baki cikin muryar kuka yace"ai ni Umma bantaɓa ganin mayaudariya irin

Huzaiyya ba Huzaiyya ta yaudareni ta gama da rayuwa ta nakuma barta da Allah ina roƙon Allah sakamin dan bazan yafeba!!!!" Aminu yace"haba yaya kadaina faɗin haka dan Allah miye rayuwar ka daure kayafe mata" da sauri yatashi zaibi Aminun Umma ta fara tafa hannu tana magana"Sahbi anya kuwa Sahbi kanka ɗaya kuwa ace duk kabi ka susuce saboda soyayya kasanya kanka a halin damuwa Mallam kanajinsu fa!" ta kalli Mallam Tanimu tana magana cikin damuwa cike da dako inkula yace"to yakikeso in masu !"  daidai nan kuma Adiyya tayi sallama domin angaya mata halin da Sahbi yake ciki tun bayan da ƴar uwarta ta gujeshi shine tazo dubashi

pls masoyan labarin *wani burin* littafin  kuna cewa kada Huzaiyya tayi ciki naso inyi maku labarin yadda kukeso sai dai hakan bazai yiyuba mussaman maman zahra naso girmama miradinki sai ina! bazaiyuyu ba labarinne yazo a haka🙏kumin uzuri nasan agaba zaku fahimceni ngd

_Taku mai kaunarku_
_Nanah ibrahim_

Pls comment and shared
[17/07, 17:32] JAMILA Katin: 💧💧💧💧💧
*WANI BURI*
💧💧💧💧💧
```TYPING```✍🏻

*FRIDAY ON 3/ 7/ JULY 2020*

```SPICIAL DIDECATED TO MAMAN ZAHRA AND DAUGHTER AMMI```💕Love u so much

*STORY*

Nanah

_SESION  FIVE_

…………… Kallanta  Sahbi yakeyi ko zaiga inda suka taɓata amman baiga komi ba ita kuwa ta daɗe da shiga duniyar tunani  muryarshi taji yana cewa"mujeko?" girgiza masa kai tayi ta fara tafiya alamun bataso yabita Aminu yace"yaya kabarta ninasan akwai abinda kedamun Adda Huzaiyya insha Allah komi zai huce kudawo  kuyi auranku" Allah sa " inji Sahbi ransa namasa zafi shi daman ba Mutum bane mai jurar wulakanci tun yana ƙarami  yana hakuri ne da abinda Huzaiyya take mashi dan tsananin kaunar  dayakeyimata  amman duk abinda takeyi gani yakeyi

wulaƙancine take masa bayajin tana da wani dalili.

uwaliya idan baki ƙoshiba sungumo mara kifito waje kiraba ƴa ƴan dandali amman nidai ni bandani Addiyya idan baki ƙoshiba .........haka mai kiran ƴan wasan ke rera waƙar tashan inda gaba ɗaya ƴan wasan suka hallari dandalin wasan gefe guda Inna Barira ke tambayar Adiyya yau bakifita tashe? ɗan turo baki tayi tace " yau bata zuwa!" Inna tana lura da ita tun bayan chanzawar walwalar ƴar uwarta shikennan itama ta chanza kamar ba itaba duk tashiga damuwa amman Inna ta yanke shawara tunda Huzaiyya ta isa aure yanzu tana da 14 years kawai da yayan mahaifiyarta yazo zasuyi magana ayi auran a huta da damuwar da suke ciki.

leƙawa tayi ɗakin su Huzaiyyar tace"nikam meke damunki tun randa na aikeki gidan su Sahbi sam na rasa kanki ko dan banice mahaifiyarki ba shiyasa bazaki gaya mani damuwarki ba!?" tashi Huzaiyya tayi cikin ƙarfin hali yau wata biyu da faruwar abin bayan bakin cikin abinda ya faru kuma ga canzawar lafiya tana fama da ita a hankali tace "a'a Inna banajin daɗi" Inna tace mike" damunki" tace zazzaɓi nake yawanyi cikin nuna jimami Inna tace ayya kedaman can farar masassara nayawan damunki da sauri taje ta kawo mata sassaƙe sassaƙe tace tatashi tasha sai taɗan fita dandali ta ɗan zaga cikin sa anni ko ta rage yawan nauyi jikinnata haka kuwa akayi amsa tayi tasha take kuwa cikinta ya fara murɗawa zuface taketo mata da sauri ta nufi bayin tana kwarara amai.
haka ta daure ta dauke hijab ɗinta tasanya asaman kayan fulanin dake jikinta farare masu adanja inda Inna ta zuba mata ido tana nazarinta Huzaiyya fare ce sol. duguwace tana da diri kasancewarta ga hip ga shap tana da dukiyar fulani kibarta tafi yawa a mazaune da kirji jikinta a mirje yake bata da rama kibarta ƴar daidai ta yadda ko ya ta motsa jikinta sai ya kaɗa duguwar fuskarta dauke take da manyan idanuwa farare masu matuƙar haske wani ado atsakiyarsu kamar ɗigon zaiba shiyake ƙara mata kwarjini tana da yalwar gashi wanda ayanzu haka kitse yake da irin kitsansu na fulani kwara huɗu mai ƴar star a tsakiya ƙaramin bakinta mai kalar pink wanda akullum sheƙi sai ƙara kyau yake kamar na jarirai hakoranta ƙanana ajere yas dasu masu matuƙar tsari bata da hayaniya miskilace saidai akwai hakuri da kawaici sannan bata daukar raini dayawa wasu a kauyan suna mata kallan mai girman kai wasu kuma naganin farin jinin da take dashi yasa take haka yayinda masu fajimta ke fassara alamar nasara tana ga mai nutsuwa,tsaf Inna ta gama wassafata tasan duk Huzaiyya tana da abubuwan data faɗa saidai gaskiya kwanakinanan tana gamin canji tare da ita, ta auwazi tayi da sauri korar tunanin da yazo mata domin Huzaiyya renontace tasan komi game da ita tatabbatar harga Allah Huzaiyya yarinyar kirkice.
asannu take tafiya har taƙarasa filin wasan inda suke tabada waƙe iri iri, Aminu ne ya hangota da sauri ya iso inda take yana washe baki yana mata magana sama sama suka gaisa ta nuna mashi batajin daɗi zata ɗan zaga murmushi yayi yace"to muje inrakaki ko?" haka yayi ta binta yana mata hira cikin barkwanci har saida taji gajiyar ta ware sannan yarakata har ƙofar gida sukayi sallama ya tafi abinda basu saniba duk inda sukayi Sahbi na binsu bisa ga umarnin zuciya amman bayaso yayi magana saboda ya lura yanzu Huzaiyya bata buƙatarsa shikuma bayasan ɓacin ranta.
*WASHE GARI*
idanuwansa lumshe hannayansa harɗe bisa kirjinsa magana yake amman inba a kusa dashi

kake ba bazakace wai waya yakeba domin motsinma sai ka mula da kyau zaka gane bakinsa nayi, albishir yake mata da cewar yau zai sanar da Dad ɗinsa game da maganar auransu azo tambaya ta nuna mashi farin cikinta sosai inda gaba ɗaya ranar sukajita tazo masu da ɗinbin farin ciki wanda har ƴar ƙamar dinner ta haɗa amman bata furta dalilin haɗawa ba tabarwa ranta, shikanshi Taufiq aranar yayi wa mutane dadama bajinta ba ƴar kaɗanba duk saboda farin cikin dayake ciki naganin yana gap da mallakar Sahibar ruhinsa.

*SANYIN MARAICE*

Kawu Lauwali ne cikin latsetsiyar motarsa   Camrry  mai wadatuwar ni imar sanyi Air Condition da kamshin Air frashiner wanda ya gauraye da  kamshin turaransa night feling  dole wanda yakasance a yanayin dayake ciki rayuwa ta mashi daɗi inka duba ga kuɗi ga ilimi ga kuma farfetect Family,   to amman kamar yadda tsarin rayuwa yake kowanne mutum zaka samu  a rayuwarsa akwai abinda yake damunsa to shima inyana damuwa a yanzu bai fice ɗiyar ƙanwashiba    Ramlat   tunbayan rasuwar iyayanta bata da makusanci kamarsa sosai kamarshi amman yarasa taya zai taimaketa tunda ya lura uwar riƙon tana ƙoƙari ga kuma tarin shakuwa wannan yasa yake ganin idan har ya amsheta bai kyauta ba amman yanzu yana ganin anzo wajan dazai bata gudunmawar data dace  haka ya isa ƙauyan tulunkalwa da wannan tunanin. zaune suke kamar kullum mood ɗin gidan dai ya daɗe da canzawa daga farin ciki zuwa baƙin ciki tun ranar da mummunar kaddararta ta bayyana shikenan suka sami kansu cikin mugun yanayi.

 lokacin da motar ta tsaya yaran dake biye da motar suna shafawa suna kuma kallo basuyi tunanin Kawun Huzaiyya bane domin dai ba a motar ya saba zuwa ba  futowa yayi nan yara da matasa sukayo mashi ca aaaa suna gaisawa yayinda yayi taraba masu kuɗi ƙauyan tulunkalwa ƙauyene mai tarin ni ima noman rani dana damina ga kiwon manyan dabbobi da ƙanana ga kwarirrika masu fitar da kayan lambu irinsu tumatir gwaba gwanda karas lemon tsami dana zaki da sauran kayan lambu haka weather garinma weather ce mai kyau   da tsari basu dayawan zafi kasancewar yawan ni imar tsirrai.
bayan yagama raba masu kuɗi cike da kishin kansa da manufa maikyau ga tushansa, haka yashiga cikin gidan kaitsaye inda tun kafin ya ƙarasa kamshin turaransa ya sanar da mutanan gidan isowarsa sauka mai kyau Inna ta mashi inka cire Huzaiyya sai ince maku ba wanda ya kai Inna farin cikin zuwansa domin ta matsu ayita takare dan yanke shawara ayi maganar auransu da Sahbi ko    kar azo ana cewa sunyi yaudara domin kaf ƙauyan ansan irin kaunar da Sahbi keyiwa Huzaiyya kuma itama anshaida ta aminta dashi daga baya kuwa intazo da wata magana yaudara kennan.
 bayan sungaisa  duk yana lura da Huzaiyya wadda ke sanye da riga da zani irinnasu na fulani dak blue  saban kitsan kanta wanda ya zuro guda huɗu yayi masifar fito da asirin kyauwun fuskarta wanda yanzu Inna tagama matashi    tabbas bahaka yasaba iskesuba gabansane ya faɗi kakadai Inna ta fara takurawa ƴartasa? kai bazai yuyuba domin yasan wacece Inna dole yawa yanayin dayaga Huzaiyya uzuri har yaji mike faruwa  cikin hikima da taushin harshe yace"nikam Barira sainaga gaba ɗaya gidannaku ya canza mike faruwa?"

Inna ta gyara zama bata ɓoye mashi komiba saida tasanardashi inda ta ɗora da cewa" amman ita aganinta ya kamata kawai atsaida maganar aura kada wani abu ya faru" Huzaiyya ya kalla wadda inba dan fuskartaba dake sauke dadamuwa bazaka taɓa cewa tana da damuwa aduniyarga ba domin shi sai yaga ma taƙara kyau da kwarjini yace" Huzaiyya kindainasan Sahbi yanzu?" kaita ɗaga alamar eh yace to wakikeso a gain kai ta girgiza alamar babu Kawu Lauwali ya fisar da iska yace" ok" jeki tafiya tayi inda yaba Inna hakuri tare da alƙawari yasan abinda zaiyi insha Allah

_Pls comment and shared_

_Nanah ce_
[17/07, 17:32] JAMILA Katin: 💧💧💧💧💧
*WANI BURI*
💧💧💧💧💧
```TYPING```✍🏻

*ON*

*10/ JULY/7/2020*

```SPICIAL DIDECATED TO MAMAN ZAHRA AND DAUGHTER AMMI```💕
Love u so much

_DUKA SHAFIN SADAUKARWA NE GA ƳAN KUNGIYAR HOME OF QUALITIES_

_SESION 7_

